# Surah 95: Al-Tin - سورة التين

بسم الله الرحمن الرحيم

[95:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

وَٱلتِّينِ وَٱلزَّيْتُونِ ١

[95:1] Ina rantsuwa da Attinu da Zaitun.

وَطُورِ سِينِينَ ٢

[95:2] Da Tur Sinina.

وَهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ٱلْأَمِينِ ٣

[95:3] Da wannan gari amintacce.

لَقَدْ خَلَقْنَا ٱلْإِنسَٰنَ فِىٓ أَحْسَنِ تَقْوِيمٍ ٤

[95:4] Mun halitta mutum a cikin mafi kyawon fasali.

ثُمَّ رَدَدْنَٰهُ أَسْفَلَ سَٰفِلِينَ ٥

[95:5] Sa'an nan, Muka mayar da shi mafi qasqantar masu rauni

إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمْ أَجْرٌ غَيْرُ مَمْنُونٍ ٦

[95:6] Sai dai wadanda suka yi imani, kuma suka aikata ayyukan qwarai; suna da sakamako wanda ba ya yankewa.

فَمَا يُكَذِّبُكَ بَعْدُ بِٱلدِّينِ ٧

[95:7] To, bayan haka me ya sa har yanzu kake qaryatad da addini?

أَلَيْسَ ٱللَّهُ بِأَحْكَمِ ٱلْحَٰكِمِينَ ٨

[95:8] Shin, ba ALLAH ne Mafi hikimah ba, daga masu hikimah?